Kashi na 1
Yesu
Ubangiji ne

# Biki Sabuwar Shekara

Darasi na 1



A KAN ME AKE MAGANA?

A ƙarshen darasin nan ya kamata ɗalibai su:

- Iya yabon Allah saboda sabuwar shekara.
- gode wa Allah domin amincinsa.
- shaida wa wasu amincin Allah.

ME NAKE BUKATA?

- su L.M.T.
- littafin rubuta matuni da birori
- kayan muzika
- kayan lashe-lashe in a akwai.
- a gayyato abokai.

AYYUKAN SHAKATAWA! MINTI 10

## Sujadar Yabo

Ku buɗe da yabon farin ciki da sujada.
Ku zaɓi waƙoƙin da suka danganci tsaikon amincin Allah kamar irin waɗannan:

◊ **Amincinka mai girma ne ......**

◊ **Zan raira jiye-jiyenƙan Ubangiji......**

◊ **Ka cancanta.........**

◊ **Zan kira ga Ubangiji............**

◊ **Mu bauta wa Allah Mai Iko......**



YI MAGANA A KAI MINTI 15

## "Zan yabe ka ya Allah....."

Ka yi tambaya ko menene ma'anar "yabo".
Don me za mu yabi Allah idan shekara ta kare?

Yayin da mun zo ƙarshen shekara kuma mun fara wata lokaci ne mai kyau da za mu yi shagalin biki na amincin Allah.

Yi tunani a kan wasu manyan harkoki biyu ko uku da suka faru a shekarar da ta gabata. Bayan kowane jinsin harkoki, sai ku yi addu'ar godiya a taƙaice ga Allah domin abubuwan amfani da suka faru, ku kuma yi addu'a domin canji a inda amfani bai samu ba:

a) cikin al'amuran duniya
b) cikin Afrika
c) cikin ci gaban kimiyya
d) cikin ikilisiya a duk faɗin duniya
e) cikin ɗarikarku.



KU DUBA LITTAFIN! MINTI 20

## "Ubangiji Mai Girma ne"

**Karanta Zabura 145:1-7**

1. Don me muke yabon Sunan Ubangiji?

2. Waɗanne sassa na girman Allah kowace tsara za ta iya yin bikinsa?

3. Waɗanne hanyoyi huɗu ne dabam dabam za mu iya ba da labari ga abokanmu a kan alherin Allah?

**Ku raira:** "Sunansa abin mamaki ne..."

**Karanta Zabura 145: 8-16**

4. Waɗanne sassa biyar ne dabam dabam na halin Allah da aka ambace su?

5. Wasu za su yi shakkar gaskiyar aya ta 9. Me za ka faɗa musu?

6. Yaya aka bayyana mulkin Allah a cikin aya ta 10-13?

7. Me ka gane daga aya ta 13,14? Ka ba da misali.

**Addu'a:** Mutum biyu su gode wa Ubangiji saboda abubuwan da suka samu na amincin Allah.

**Karanta Zabura 145:17-21**

8. Yaya Allah ya bayyana adalcinsa gare mu?

9. Ina abu uku da za mu yi?

10. Mu raira waƙar yabo ga Allah, amma waɗanne hanyoyi ne za mu iya yin "magana cikin yabon Ubangiji"?

**Ku raira:** "Ubangiji Allah
Kai ne farkon kome
Tun da farin hasken safe
Muna neman ka....."

APPLICATION ACTIVITY 15 MINUTES

## Zan faɗa .....

Ka sa mutum biyu ko uku su ba da labarin abu guda musamman da suka taɓa samu na amincin Allah a cikin shekara da ta gabata.

Bayan kowanne ya gama, sai ku bi da gajeruwar addu'ar godiya.

Ta wace hanya za ku iya morar abubuwan da kuka samu don ku faɗa wa wasu labarin alherin Allah da amincinsa?

Ka rubuta abubuwan da ka samu cikin ɗan littafinka na rubuta matuni a cikin makonni masu zuwa. Yana da taimako don a iya duba baya a karanta abin da Allah yake yi a cikin rayuwarka.

Ka sa 'yan ƙungiya da dama su zaɓi waƙoƙin sujada da suka danganci amincin Allah, suna ba da dalilin zaɓensu.

Ku ɗauki lokaci kuna zumunci da juna ku kuma san sababbin mutanen da suka zo.

Ku ji daɗin lashe-lashen wartsakewa da aka shirya idan akwai.

Ku rufe da addu'a kuna bayyana dogorarku ga Allah domin amincinsa cikin shekara mai zuwan nan.



**Ku je ku faɗa wa wasu labarin alherin Allah da amincinsa.**

### AIKIN GIDA NA WANNAN MAKO:

Ka fara sabon shafi a cikin ɗan littafinka na rubuta matuni.

Ka lasafta hanyoyin da ka samu amincin Allah a cikin shekaran nan da ta wuce.

Da kake karanta wasu ayoyi kima na wannan Zabura kowace rana, ka rubuta sheɗara guda a kan abin da Allah yake faɗa maka.

**Rana ta 1.**
Zabura 145:1-3

**Rana ta 2.**
Zabura 145:4,5

**Rana ta 3.**
Zabura 145:6,7

**Rana ta 4.**
Zabura 145:8,9

**Rana ta 5.**
Zabura 145:12,13

**Rana ta 6.**
Ka haddace:
Zabura 145:13b,14.